# Gina Hanyar Sadarwarka Ta Al’umma Masu Rajin Kawo Sauyi

Mahalarta taron za su koyi yanda hanyoyin sadarwa zamani ke inganta ƙoƙarin wayar da kan jama’a. Haka kuma mahalarta taron za su koyi yanda ake samar da abubuwa a don yaɗa bayanai game da wani sanadin da ake sha’awa.

# Yin Amfani da Hanyoyin Sadarwar Zamani don Rajin Kawo Sauyi

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Akwai wata fitacciyar yankin jimla da ke cewa, “ba a kan abin da ka sani ba ne. A kan wanda ka sani ne.” Yayin da ba a gaskata wannan 100 bisa 100 ba (abin da ka sani shi ma ba shi da muhimmanci!), tunatarwa ce mai taimakawa wajen sanin muhimmancin hanyar sadarwar.

Ko kana neman aiki ko kuma kana yin ƙoƙarin buga wasannin motsa jiki a mataki na gaba, samun hanyar sadarwa mai kyau zai iya taimaka maka wajen tuntuɓar wanda zai taimaka maka wajen cimma manufarka. Ƙoƙarin wayar da kai ba shi da bambanci. Girma da ingancin hanyar sadarwar mutanen da muka sani, shi ne samun sauki wajen ƙirƙirar canji a cikin al’ummarmu.

Daga iyalanmu da abokanmu zuwa malamanmu da shugabannin al’ummu, mun san mutane fiye da yanda muka yi tunani, musamman idan muka haɗa da abokan abokai sannan muka faɗaɗa hanyar sadarwarmu ta zarce waɗanda ke kusa da mu. Waɗannan mutanen za su iya zama mutane masu jajircewa wajen cimma manufarmu.

Akwai mutane da yawa da ba mu riga mun san su ba da za su taimaka wajen cimma manufarmu. Dandalin sadarwar zamani da intanet na ƙara faɗaɗa gabatar da wasu hanyoyin haɗuwa da irin waɗannan mutanen da za su iya taimakawa da fasaha ko kayayyakin aiki ga ƙoƙarinmu na rajin kawo sauyi.

## Kashi Na Biyu

A kan allon majigi a gaban ɗakin, nuna wani misalin bidiyo aka daidaita da / mahalarta taronka na cikin gida / yanki don nuna yanda aka haɗa mutane ta hanyoyin sadarwar zamani da kuma yanda za mu ci moriyar waɗannan haɗe-haɗen.

### Tambayi Ɗalibanka

Ta yaya za a yaɗa bayanai da kyau ta hanyoyin sadarwar zamani da ake da su?

Ta yaya za mu yi amfani da waɗannan mutanen don inganta ƙoƙarin kawo sauyi?

### Sanar da Ɗalibanka

A cikin waɗannan ayyukan, za ka ƙirƙiri bayanan da za a iya rabawa ta intanet da ke fayyace sanadin da ka damu da shi. Da zarar ka raba ƙoƙarin rajin kawo sauyinka a

intanet, za ka iya sanar da wasu game da abubuwan da ka damu da su sannan kuma ka samu ikon haɗuwa da sababbin mutanen da za su iya taimakawa ƙokarinka!

# Aiki

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Ƙirƙiri wasu abubuwan da za a iya rabawa ta intanet (misali., ta hanyar yin amfani da Daftarorin Google, dandalin sadarwar zamani, shafin yanar gizon Wordpress, shafin yanar gizo a kan Neocities, gabatar da wani majiga ta hanyar yin amfani da Scratch, da dai sauransu.) game da wata matsalar da ka damu da ita, a inda ka:

1. Rubuta wata gabatarwa kana mai yin bayani a kan sanadin da kuma dalilin da yasa ka yi imani cewa yana da muhimmanci.

2. Samar da kafafen shafukan yanar gizo da yawa (misali., wata maƙala a intanet) da aka sadaukar ga matsalar.

3. Jero sunayen mutane uku waɗanda suka rubuta, shafin yanar gizo, tweet, ko suka samar da abubuwan watsawa ta hanyoyin sadarwa game da wannan yankin. (Ba tilas ba: Idan za ka iya, rubuta tweet ga kowane ɗaya daga cikin waɗannan mutanen sannan ka sanar da su game da sanadinka da kuma abun da kake so ka cimma.)

### Tattaunawa a Aji

Ba mahalarta taron mintuna 30 domin su kammala ayyukan. Ya danganci lokacin da aka bayar, a cikin wannan ƙungiyar ta yanzu ko kuma ta biyun da aka ƙaddamar, nemi mahalarta taron domin su raba abubuwansu da ƙungiyoyin masu yawa sannan ka yi tattaunawa ta mintuna-15 kana mai yin bayani a kan hanyoyin.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.